# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na huɗu: Kwallon ƙafa na kowa ne


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya tace: | Ludger Schadomsky da Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| Metogba | ɗan shekara 28, ƙwararren ɗan wasan ƙwallon ƙafa |
| Mr. Madu | ɗan shekara 54, shugaban ƙungiyar wasa ƙwallon ƙafa ta ƙasa |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| John: | ɗan shekara 15 |

**MAI GABATARWA**:

Jama'a, barkanmu da warhaka da kuma sake saduwa da ku a cikin wani sabon shiri na "Ji Ka Karu", wanda muke kawo muku a kan wasan ƙwallon ƙafa a nahiyarmu ta Afirka. A cikin shirin da ya gabata, Zakari ya buga ƙwallonshi har ta fasa wani taga. Metogba kuwa, wato ƙwararren ɗan wasan ƙwallon ƙafan nan, ya yi bayani ne a kan muhimmancin gasar da zai gudanar. Ita kuma Safina, wadda take da sha'awar yin wasan ƙwallon ƙafa, ta gano cewa tunanin da take yi wa antinta da ke zaune a birni, ashe abin ba haka yake ba. Yanzu sai ku biyo mu sannu a hankali don jin yadda shirin zai kasance a yau, kuma za mu fara ne daga irin halin da Zakari ya samu kanshi a ciki bisa dalilin fasa tagar wani da ya yi.

**Fitowa ta 1: A gidan Anti Lily**

Safina, Zakari

**SAFINA:** A taimake ni! Anti, ki taimake ni! Wayyo jama'a, ku taimake ni! Anti! Ɓarayiii! Wane ne? Me kake nema daga wurina? A'a, ƙwallo? Ina ganin wani ne ya bugo ƙwallonshi har ta faɗo nan. Wayyo ni Allah! Yanzu wane irin bayani zan yi wa Anti idan ta dawo? Dole in ajiye ƙwallon nan. … Bari in yi hankali kar in yanke kaina. Yauwa, gara ma da yake ina sanye da takalmana, bari in gani ko wane ne. … Kai! Kai, da kai nake! Kai ne ka fasa mana taga?

**ZAKARI:** Uhmm, e ni ne, amma wallahi ba da gangar na yi ba. Ko za ki taimaka ki dawo min da ƙwallona, don Allah?

**SAFINA:** Mene!? A'a, ka yi haƙuri, zan ajiye wannan ƙwallon har sai antina ta dawo gida. Dole ne in san irin bayanin da zan yi mata game da yadda aka yi tagar nan ta fashe.

**ZAKARI:** Ke, ki saurare ni ki ji! Ba na son in yi wata rigima da ke

yarinya. Na riga na ba ki haƙuri bisa abin da ya faru. Ki jeho mun ƙwallona, ko kuma in zo in karɓa da kaina ne!

**SAFINA:** Kana ba ni tsoro ne? To bari in ba ka labari. Ba na tsoronka ko kaɗan! Kuma ka san cewa ni daga ƙauye nake, saboda haka ba wannan ba ne karo na farko da na fara haɗuwa da yara irinku marasa kunya. Wannan ƙwallon tana nan, har sai antina ta dawo.

**ZAKARI:** Ina ganin na san antiki. Antinki mutuniyar kirki ce, ba zan damu ba. Kin ga, wannan ba shi ne karon farko ba da haka yake faruwa. Muna buga ƙwallo, mu fasa tagogi, sannan mu ba da haƙuri. Haka yake faruwa ko da wani lokaci.

**SAFINA:** Wataƙila, amma ni a wurina, wannan shi ne karo na farko. Kai wane irin ɗan ƙwallo ne ma? Ba ka lura da inda za ka buga ƙwallon ba ne?

**ZAKARI:** Kin fa wuce gona da iri! 'Yar yarinya da ke. Me kika sa ni game da ƙwallon kafa?

**SAFINA:** Ummm… To shi ke nan, mu yi bugu biyar biyar na bugun daga kai sai mai tsaron gida. In ka cinye, ka ɗauki ƙwallonka, in kuma ni na cinye, in riƙe ƙwallon, kai kuma ka zauna nan har sai antina ta dawo gida. … Ba ta tsaya nan ba. Sannan kuma ka yi wa antina bayanin abin da ya faru. Ka shirya?

**ZAKARI:** Wai da gaske kike yi?

**SAFINA:** Ka ga ina murmushi ne?

**ZAKARI:** A'a. Ina tunanin cewa, me ya sa kike ɓata wa kanki lokaci ne

haka? Ba zai fi miki sauƙi ba, ki ba ni ƙwallona kawai, maimakon ki ɓata wa kanki lokaci na ɗaukar *shot* masu wahala? To shi ke nan, ina jira.

**MAI GABATARWA:**
Zaks ya tabbata da cewar wannan zai zama wasan yara ne, sai dai bai san irin wadda yake tare da ita ba ne. Saboda haka cikin sauri, sai Safina ta gangaro ƙasa don su yi wasan bugun daga kai sai gola da Zakari. A halin da ake ciki kuma, Metogba na cikin ranarshi ta farko a wajen gasar zakulo 'yan wasa. Amma abin da ya ba shi mamaki…

**Fitowa ta 2: A babban filin wasa**

Metogba, Mr. Madu

**METOGBA:** Me yake faruwa ne? Yanzu mun kai awa ɗaya a nan, amma kuma waɗanda suka zo su, a'a … ɗaya, biyu, uku, huɗu, biyar, shida, bakwai, takwas. 'Yan wasa takwas kawai!

**MR. MADU:** Gyara! Biyar dai, 'yan wasa biyar ne kawai. Ukun mata ne.

**METOGBA:** Wai kai wane ne ma ka ce?

**MR. MADU:** Sunana Madu, shugaban ƙungiyar shirya wasan ƙwallon ƙafa ta ƙasa.

**METOGBA:** Haka ne? Ina mamakin yadda aka yi ka samu wannan aiki.

**MR. MADU:** Me ka ce?

**METOGBA:** Kar ka damu. Ina so ka gane abu ɗaya. Wannan gasar, ba za a nuna bambanci ba ga mata, saboda kawai suna mata. Wasan ƙwallon ƙafa ya wuce yadda kake tsammani. Kalmar

FIFA na nufin ƙungiyar shirya wasan ƙwallon ƙafa ta duniya. Zan fassara maka da wata manufa, wato ƙwallo-ta-kowa-da-kowa ce. Kowa! Haka ya haɗa da mata, nakasassu, matasa, tsofaffi, masu arziki, da kuma talakawa. Idan dai har za ka iya gudu kuma ka buga ƙwallon, ya kamata a ce kowa yana jin daɗin ƙwallo!

**MR. MADU:** Gaskiya da ni ban taɓa kallonta ta wannan sigar ba. Amma dai kai ka shirya gasar. Ni na zo ne kawai don in taimake ka. Muna iya farawa?

**METOGBA:** E, ba tare da wani ɓata lokaci ba. … Ina ma kowa maraba da zuwa wannan wuri. Da farko dai za mu fara ne da gabatar da kanmu kamar yadda aka saba. Ka faɗa min sunanka, shekarunka, da kuma dalilin da ya sa kake so ka shiga wannan gasa. Ku tuna, kar ku yi min ƙarya. Idan ka yi, kuma na gane, to zan kore ka. Kowa na iya farawa.

**SHEHU:** Ni sunana Shehu, shekaruna… amma, a gaskiya ban san ko shekaruna nawa ne ba. Ina so in shiga gasar ne saboda ina ganin cewa, ita ce kawai hanyar da rayuwata za ta kyautata nan gaba.

**METOGBA:** Daga ina ka fito, Shehu?

**SHEHU:** Ni ba ni da wani takamaiman gida. A titunan birnin Gabas kawai nake yawo.

**METOGBA:** To yanzu kana da gida. Waɗannan su ne sabbin 'yan'uwanka. Ina yi maka maraba da shigowa ƙungiyar. Na gaba!

**MAI GABATARWA:**

Mai sauraro na san cewa za ka yi mamakin wannan abu. Yaya za a yi Shehu ya yaudari babban abokinshi, sannan ya kashe mishi gwiwa dangane da wannan gasar fid da gwani, bayan shi kuma ya shirya zai je wurin gasar? Amsar wannan tambaya dai mai sauƙi ce. Yana tsoron yin takara da abokin nashi. A yayin da sauran ’yan wasan suka ci gaba da gabatar da kansu, daga gaba kaɗan, a filin wasan nan mai ƙura, Zakari ya shirya don ya yi bugunshi na farko a gasarsu da Safina, wadda take tsaye a tsakiyar wasu manyan duwatsu biyu, don ta tare bugun daga kai sai mai tsaron gida.

**Fitowa ta 3: A filin wasa mai ƙura**

Zakari, Safina

**ZAKARI:** Na so a ce Shehu yana nan domin ya ga yadda zan yi. Allah kaɗai ya san inda yake.

**SAFINA:** Za ka bugo ƙwallon, ko kuwa za ka ci gaba da cika baki ne?

**ZAKARI:** Na shirya! Ga cina nan na farko! … *Gooaaal!!!* Na gaya mi ki, wannan abu ne mai sauƙi. Yanzu saura ke ki bugo.

**SAFINA:** To shi ke nan. Ka shirya? Bari in bugo.

**ZAKARI:** E, ko in rufe idona ne?

**SAFINA:** *Gooaaal!!!*

**ZAKARI:** Kai, kai, kai, kai! Yaya kika yi? Ɗan tsaya! Yaya aka yi kika yi?

**SAFINA:** Ɗaya da ɗaya. Saura kai.

**ZAKARI:** Shi ke nan, na ga kina nema ki raina ni? Amma dai kin ga ina yi miki da wasa ne, amma yanzun nan zan nuna miki ko

ni wane ne a harkar ƙwallon ƙafa.

**SAFINA:** *Yeeeah!!!!* Na tare! Saura ni.

**ZAKARI:** Kai! Me nake gani! Mace? Ta tare buguna? Lalle ni sakarai ne, ba ni da wani amfani. Shehu ya yi gaskiya. Ko da na je wurin gasar nan ma ba zan taɓuka kome ba.

**SAFINA:** Gasar ƙwallo? Wane irin gasar ƙwallo?

**ZAKARI:** Ba ki da labari? Metogba na haɗa gasa don zaɓen 'yan wasan da za su zagaya ƙasashen Turai.

**SAFINA:** Metogba? A ina? Don Allah ka kai ni wurin da ake yi. Ban san garin nan ba sosai.

**ZAKARI:** A'a, wannan wurin ba wurin zuwa mutane ne kamarki ba ko kamata. Bayan haka ma ai kin ce antinki ta kusa dawowa.

**SAFINA:** E, amma ai ba za mu daɗe ba. Ina so ne in ga Metogba kawai ka ji. Don Allah mana. Af, ni sunana Safina.

**ZAKARI:** Ni sunana Zakari, amma Shehu na kirana Zaks.

**SAFINA:** Shi ke nan. Mu yi sauri kafin antina ta dawo, zo mu tafi!

**MAI GABATARWA:**
Shi ke nan, yanzu Zakari da Safina sun zama abokanai, kuma sun kama hanyarsu ta zuwa babban filin wasa na garin, ba tare da sanin abin da za su taras a can ba. A lokaci guda kuma, shi ma John ya kama hanyarshi zuwa filin, sanye da kayan wasa sabbi na wata mashahuriyar ƙungiyar ƙwallon ƙafa ta ƙasashen Turai.

**Fitowa ta 4: A babban filin wasa**

John, Metogba, Zakari

**JOHN:** *Coach* Metogba. Ka yi haƙuri, na zo a makare.

**METOGBA:** Yau zan ƙyale ka. Amma kar ka sake. Kowa ya saurare ni! Wannan shi ne…

**JOHN:** John…John Gambo.

**ZAKARI:** Gambo? Gidan iyalin Gambo? Kana nufin Honourable Gambo?

**METOGBA:** John ɗan wani ɗan majalisar dokoki ne, amma a nan, duk ɗaya muke, ba wanda ya ɗara wani. Ba wani bambanci a cikin fili tsakaninsa da kowane ɗaya daga cikinku. Ko akwai wani daga cikinku da ya san dalilin da ya sa yara da yawa ba su zo ba? Na sa ran ganin cewa wurin zai cika maƙil.

**SHEHU:** Wataƙila saboda yawancin yara sun tafi aiki ne a ƙauyuka, a cikin birni, kuma wasu har yanzu suna cikin ahm… daji.

**METOGBA:** A cikin daji?

**JOHN:** *Coach* Metogba, ina ganin abin da yake nufi shi ne cewa, yawancin yaran suna can tare da ƙungiyoyin 'yan ta'adda a cikin daji. Suna ƙoƙarin su hamɓare gwamnatinmu.

**METOGBA:** Afirka! Wai yaushe ne za a bar yara su kasance a matsayinsu na yaran? Ba kome, mu fara jijjiga jikinmu. Mu zagaye fili sau biyar, sannan in mun gama, mu haɗu a tsakiyar fili. To, to, to, mu je,mu je, mu je!

**MAI GABATARWA:**

Metogba ya yi magana mai ƙarfi. Muna da matasa da yawa masu basira, waɗanda manyan 'yan kasuwa, ko shugabannin ƙungiyoyin ta'adda kan yi amfani da su wajen biyan buƙatun son zuciyarsu, ta hanyar sa su a ƙungiyoyin ta'addanci, har su koma suna yaƙar jama'ar ƙasarsu ta Afirka. Yaya za mu yi mu dawo da su don su koma su ci gaba da rayuwa mai inganci, su bi irin rayuwar da suke ganin za ta fisshe su? Da waɗannan tambayoyin kuma muka kawo ƙarshen wannan shiri na "Ji Ka Karu" na yau. Sai a kasance da mu a shiri na gaba domin jin yadda za a sadu da Zakari da Shehu a wurin gasar. Idan kuma ana so a ƙara saurararon wannan shirin, sai a neme mu a adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.